# 1 Taƙaitaccen Bayani A Kan Aikin Hajji

## Makka

Suna ne da aka tsago shi daga kalmar "Bak" wadda take nufin kwari da yaren samiyyah.

## Abubuwan Da Ke ciki

Makkah A Da Da Yanzu
Falalar Makkah
Hukunce-Hukuncen Da Suka Keɓanci Makkah Da Masallacin Harami
Ka'abah Mai Girma
Wuraren Aikin Hajji

Sunan Makkah ya zo da lafazin Bakkah, a cikin Faɗin Allah Maɗaukakin Sarki {Haƙiƙa farkon ɗakin da aka sanya wa mutane a bayan ƙasa shi ne wanda yake a garin Bakkah, mai albarka da kuma shiriya ga talikai} [Albaƙara : 96].

Tarihin Makkah yana kowama wa zuwa ƙarni na sha tara kafin haihuwar Annabi Isa (A.S) zamanin Sayyidina Ibrahim da Isma'il (A.S) waɗanda su ne farkon waɗanda suka zauna a cikinta, Allah Ta'ala yana bamu labarin Annabi Ibrahim inda yake cewa {Ya Ubangiji na zaunar da zurriyata a wani kwari wanda ba shi da shuka wajen ɗakinka mai alfarma. Ya Ubangiji ka sanya zukatan mutane su riƙa karkata zuwa garesu saboda su tsaida sallah, ka azurta su da 'ya 'yan itace ko sa yi godiya} [Ibrahim : 37]. Saboda falalar addu'ar Annabi Ibrahim ruwan zamzam ya ɓuɓɓugo daga ƙarƙashin ƙafar Isma'il (A.S) lokacin da ruwa da abinci suka ƙare wa mahaifiyarsa Hajara, to tun daga wannan lokaci ƙabilu suka yi tururuwa zuwa wajen wannan ruwa, rayuwa ta miƙe a cikin wannan gari.

Kabilu suka ci gaba da cincirondo da taruwa a wannan wuri, har lamarin ya kai ƙuraishawa sune suke mulkin garin. Haka ƙuraishawa suka ci gaba da lura lamarin garin har zuwa bayyanar Manzon Allah (S.A.W), wanda ya canza rayuwar Makkah da ma duniya gaba ɗaya.



https://www.al-feqh.com/ha